Ƙungiyar ƙasar Japon mai kula da hulɗar ƙasa da ƙasa

Ma'aikatar Ministan aikin gona

# Binciken dausayoyin yankin Sahel a jamhuriyar Nijar




## Littafin horo bisa tsarin tashi da kanƙa, da kafa ƙungiyoyin ci-gaban gari (CVD) ta hanyar demokaraɗiya.

Na mahalarta.

Oktoba 2006

Ƙungiyar ƙasar Japon mai kula da albarkar tsanwa (J.Green)

Wallafawar daga ƙungiyar ADA cikin yarjejeniya tare da EDOS.

# Abubuwan da suke ciki

Gabatarwa ........................................................................... 3
Gurorin wannan littafin ............................................................... 4
Mataki na farko: Saduwa ta bayar da bayani tare da hukumomin gargajiya. . 5
Mataki na biyu : babban taro na farko, na shirya zaɓe. ............................ 5
Mataki na 3 : Shirin kayan aiki a jajibirin ranar zaɓe. ............................ 14
Mataki na 4: Taron babbar majalisar zaɓe............................................ 14

# Gabatarwa

Wannan littafi  na horo bisa tsarin tashi da kanka, da kafa ƙungiyoyin ci-gaban gari (CVD), wata fusa'ar koyo ce, wanda aka wallafa, saboda malaman da suke kula da tafiyar da zaɓen biron CVD. Waɗannan malaman, suna da nauyin waye kan al'umma, kuma da su kama mata cikin tafiyar da zaɓen.

Don haka, ya kamata su iya tsara, kuma su iya yin shugabancin tafiyar da zaɓen biron CVD tare da ƙwarewa. Wannan littafin ya ƙumshi wani yawan matakai, wanɗanda malaman za su bi,don su koyar da abubuwan da suka koya su ma.

# Gurorin wannan littafin

Littafin horo bisa tsarin tashi da kanka, da kafa ƙungiyoyin ci-gaban gari (CVD), fusa'a ce ta koyarwa, wadda za ta sanya kowanne malami ya koyar da abubuwan da ya koya shi ma.

Ga gurorin littafin:

Ya sulfanta ma malamai cikin bayar da bayanin bisa ma'anar :

- Tsarin tashi da kanka;
- Kundin ƙa'idodin ƙungiya;
- Zaɓe na inci kai, da ta hanyar demokaraɗiya;

- Sulfanta zaɓen biron CVD ta hanyar demokaraɗiya.

## Mataki na farko: Saduwa ta bayar da bayani tare da hukumomin gargajiya.

Baya dubun gaisuwa da fatar alheri zuwa ga hukumomin gargajiya (Maigari da fadarshi), malamin ya kwatanta masu gurin horo da ya samu. Kuma ya kwantanta masu hujjojin da suka sanya aka zaɓi daraktocin makarantu, da mushunan gona, da wakillan gari, da kuma masu faɗi a ji. Bayan haka, ya tambayi hukumomin su tsaida ranar taro da dukan illahirin mutanen garin.

**A yi la'akari !** : ya kamata malami ya kula da a tsaida rana, da kuma lokacin da mutane da yawa suke iya zuwa. Ya yi la'akari, don dukan ƙungiyoyin garin, da kuma dukan ma'aikata su wakilta. A ɗauki matakai don dukan rukunan al'umma (mata, da matasa, da makiyaya, da ma'aikatan hannu, da manoma, d.s.) su halarta da yawa. Kuma a ɗauki matakai don kowa ya samu wuri.

Daraktocin makarantu, da mushunan gona, da wakillan gari, kuma da masu faɗi a ji suna da matsayi mai mahimmanci cikin ci-gaban garuruwa. Suna iya taimakawa da gaske ga tafiyar da kafa CVD ta hanyar demokaraɗiya, saboda waɗannan hujjojin da dama :

- Suna bayar da horo kuma suna da fusa'ar koyarwa sosai;
- Ba su goyan bayan. Ba su shiga cikin ra'ayin mutanen gari ko cikin wata matsala ;
- Daraktocin makarantu ,sun ƙware ga ƙafa ƙungiyoyin makarantu (COGES). Bayan haka suna cikin COGES, kuma sun san yadda ake kafa CVD.

## Mataki na biyu : babban taro na farko, na shirya zaɓe.

1) Ya kamata malami ya zama cikin mutanen farko masu isowa wurin taron, don ya duba tsarin wurin zama, kuma ya tarbi mahalartan.
2) Malami ya tambayi mai gari, ya faɗi gurin taron. Idan kuma akwai wani ƙarin bayani sai malamin ya yi shi.
3) Malami ya fara da ma'anar tsarin tashi da kanta, cikin yana gwada ma mahalartan hoto mai lamba 1 na shafi 7. Ya tambaye su abin da suke gani bisa hoton. Sa'an nan sai ya tambaye su, su faɗa mashi karin magana da ya dace da hoton. Ya taƙaice hirar, kuma ya ba su bayani bisa tsarin tashi da kanka ta waɗannan sheɗaru na wannan matanin :

Tsarin tashi da kanka fusa'a ce, inda wasu mutane, masu wata matsala iri ɗaya suke nazari, don su gano da babbar hujjar matsalar. Waɗannan mutanen suna tsara aikace-aikace. Cikin lokacin farko ,suna aikata su da ƙarfin kansu ,da kuma kuɗin kansu. Waɗannan mutanen suna ɗaukar nauyin cin nasara ko rishin cin nasara na aikace-aikacen.

Malami ya gwada ma mahalartan hoto mai lamba 2 na bisa shafi 8, ya tambaye su abin da suke gani, kuma da karin magana da yake rubuce bisa hoton. Malami ya taƙaice hira kuma ya faɗi da cewa, shi makiɗi da mai rawa yana nuna tsarin tashi da kanta, tamkar hanya ce wanda yake ita kaɗai ce da mutanen ƙauye za su bi don su kyautata zaman rayuwarsu.



Hannu ɗaya ba ya ɗauka ɗaki.



Hoto na 1






Idan kidi a canza, rawa ma canzawa take yi

4) Malami ya tambayi mahalartan, su zana mashi aikace-aikacen da mutnen gari suke iya yi da ƙarfin kansu,da kuma kayansu ,don su kyautata zaman rayuwar gari. Ya taƙaice hira, kuma ya faɗa masu wasu aikace-aikace da ba su zana ba kamar:

- Tsabta (shara, cira ko noman haki cikin gari d.s)
- Cikon ramun hanyoyin da suke ratsa gari, da ruwa da suke kwantawa tsakanin ɗakuna, da gidan magani na gari.
- Gina masallaci, da ajin makaranta, da gidajen malamin makaranta, da kuma gidan magani.
- Dasa itatuwa.
- Haɗa akwatin magani na makaranta.
- Gyaran ɗakunan tsohin mutane waɍɗanda ba su da kowa.

5) Malami ya tambayi mahalartan abin da ya kamata a yi, don dukan mutanen gari su sa hannunsu cikin waɗannan aikace-aikacen. Ya taƙaice hirar kuma idan ya dace ya faɗi da cewa:

| |
|---|
| Idan ana son waɗannan aikace-aikacen su aikatu, ya kamata mutanen gari su tsara kansu, su kafa wata ƙungiya mai haɗin kai mai suna kwamitin ci-gaban gari (CVD). A aza wani ɗan gungun mutane wanda kowa ya yarda da shi, don su tsara, su aikata, su bi-sau-da ƙafa ,kuma su mizanta fasalin ci-gaban gari (PDV) wanda babban taron gari ya amince da shi. |

Ya kamata malami ya ƙarfafa faɗin halayen kwamitin ci-gaban gari. Haka shi CVD ɗin, ya kamata:

- **A wani gari:** ya iya faɗin ra'ayinshi, ya iya faɗi aji, a iya amince da matsayin shi, ya iya tattamna da abokan hulɗa kamar da hukuma, da ƙungiyoyi, da ƙungiyoyin taimako na hulɗar ƙasa da ƙasa.
- **A cikin gari**: ya iya yin lissafi, ya iya yin nazari, ya iya tsara kanshi kuma ya iya zaɓen shugabanin da yake so.

6) Malami yana yin bayan, cikin yana gwadin wannan hoton jikin mutun tamkar kwatanci da sassan kwamitin ci-gaban gari.
   - Kai, yana tamkar babban taro na kwamitin gari: shi ne sashe na ƙoli, inda ake ɗaukar dukan matakai.
   - Ciki ,yana tamkar biron kwamitin ci-gaban gari: shi ne « motar » ɗin na ci-gaba.

- Hannuwa da ƙafafuwa, su ne tamkar tayoyin huɗu na kwamitin gari : su ne tamkar ƙananan kwamitocin gari. Ci-gaban gari ya dogara ga tayoyin huɗu na ci-gaba, waɗanda suke su ne : isasshiyar cimaka, da lafiya, da horo da kuma hali na kuɗi.
- Idanu da kunnuwa su ne tamkar masu bincike na kwamitin gari. Suna lura, suna bincikawa, kuma suna kai bayani zuwa ga babban taro.

7) Malami ya tambayi mahalartan, mi ne yake tsakanin sassan daban-daban na CVD. Ya taƙaice, kuma ya kwatanta ,tare da zanantawa, hulɗar aiki da ta girmantaka da ke akwai tsakanin sassan na kwamitinci-gaban gari.




8) Malami ya gwada ma babban taro takardun shirin ƙa'idodin ƙungiya, kuma ya faɗi amfanin waɗannan takardun. Ya ƙarfafa kwatanta ma kwamitin ci-gaban gari, mahimmancin samun takardar amincewa, don su tafiyar da aikace-aikacensu. Kuma ya kwatanta amfanin wannan takardar amincewa, da takardun da za a haɗawa don a same ta, da kuma kai-da-kawo da ake yi.
9) Malamin yana kama ma mahalartan, cikin cin gyaran takardun shirin kundin ƙa'idodi. Bai kamata ba ya sanya ra'ayinshi, ya yi wani rinjaya cikin tsarin tafiyar ƙungiyar. Ana nuhin, kar ya ɗauki wata niyya maimaikin mutanen garin. Ya kama masu kaɗai,

kuma ya shawarta masu, su tsaida ƙa'idodin da suka ga sun fi dacewa da tafiyar ƙwarai ga ƙungiyar.

10) Malamin ya bayar da misalin wani biro da ba ya aiki, saboda shugaban kaɗai ne yake aiki, kuma ba a ganin kingin mambobin. Ya tambayi mahalartan mine ne ya kawo wannan abin. Mahalartan za su bada amsa, sai malam ya taƙaice. Idan ya dace, ya bayar da irin waɗannan mafaran: ana aza wasu cikin biro tilas, kenan ba da son mutune ba ake sa su, yin takara ba, koko mambobin ba su san ko mine ne aikinsu ba.

11) Malam ya tambayi ire-ire zaɓe, da amfanin kowane irin zaɓe, kuma da cikas ɗin kowanne, tare da ya yi aiki da wannan allon.

1. Ire-iren zaɓen mambobin biro na wata ƙungiya

| Irin zaɓe | Kamannu zaɓen | Amfaninshi | Cikas ɗin shi |
|---|---|---|---|
| Na ɗaga hannu | Masu zaɓen da suke son wani ɗan takara, sai su ɗaga hannu, sa'an nan a yi ƙilgo. Idan masu takaran da yawa ne, sau ɗaya mutun yake iya yin zaɓe. Idan yawan masu zaɓe ya zo daidai ga masu takaran farko biyu, sai a sake wani zaɓe don a raba gardama. | -Yana sa a yi zaɓen ƙwarai<br>mutanen garin sun fi saurin gane shi ;<br>-ba ya da wuyar tsarawa. | -yana iya kawo wasu matsaloli<br>-Tsoron jama'a ko tsoron ɗan takarar da ba a zaɓa ba. |
| Na jerawa bayan ɗan takaran da mutun yake so. | Masu zaɓen suke jerawa bayan ɗan takaran da suke so. | -Ba ya da wuyar ganewa wurin mutanen gari.<br>mutanen gari suna saurin ƙwarewa cikin shi. | -Yana iya kawo wasu matsaloli<br>-Tsoron jama'a, ko tsoron ɗan takaran da ba zaɓa ba. |
| Na zamne tsaye | Masu zaɓen da suke son wani ɗan takara sai su tashi tsaye, sa'an nan a yi ƙilgo. | | -Yana iya kawo wasu matsaloli<br>-Tsoro jama'a, ko tsoron ɗan takaran da ba zaɓa ba. |
| Na yarjejeniya | Masu zaɓen suna shawara su ɗauki ɗan takara guda. | Ba ya da wuyar ganewa, kuma ba ya da wuyar tsarawa. | -yana iya kawo wasu matsaloli.<br>-Ba kullum yake barin a zaɓi wanda ya dace ba. |
| Na ƙura'ar ɓoye | Ana ba kowane ɗan takara takarda mai launi daban (koko wata shaida) sa'anan, sai masu zaɓe su ɗauki takardar ɗan takaran da suke so, su jefa ta cikin akwatin ƙura'a. A ƙarshen zaɓe sai a yi ƙilgon ƙuru'o'i. | -Yana tsare asirin zaɓe<br>-Yana sanya a zaɓi wanda ake so ba cikin damuwa ba<br>-Yana kare jittuwa tsakanin mambobi da masu takara. | -Yana da wuyar ganewa ga mutanen gari.<br>-Yana da neman shiri na hali (akwatin kuru'a da takardun zaɓe; d.s.) |

Malami ya ƙarfafa kwatanta mahimmancin zaɓe ta hanyar demokaraɗiya ,kuma ya gwadi dacewar da yin zaɓe mai aiki da inci, kuma maras maguɗi.

12) Malami ya ƙara gwadi ga karo na biyu, matsayin mambobin biron CVD, kuma da aikin kowane mamba.

13) Ta hanyar ƙaramar wasar kwaikwayo, malami ya yi bayani a kan sharuɗɗan zaɓen mambobin biron CVD. Ya nemi mahalartan da za su iya wasar kwaikwayon.

A lura: Malamin ya ƙarfafa faɗin sharuɗɗa da ya kamata a samu, don a zama shugaba,da ma'ajin kuɗi, da masu taimaka masu. Haka su ma masu bincike ,sai sun cika irin waɗannan sharuɗɗan na mambobin biro.

Kwatanci

Karamar wasar kwaikwayo ta farko

| |
|---|
| Shugaban biron kwamitin ci-gaban gari, ya gayyaci taro, don a tattamna bisa tsabtar gari, saboda ɗauɗa ta yi yawa a cikin gari. Wani mamba ya ce yana da magana. Ya ce : «Ni, ba za ni iya shiga cikin ayyukan tsabtar gari ba ,saboda za ni tafiya Tawa wurin wani aiki». Wani mamba kuma ya tashi tsaye ya ce : «Duk ƙarshen sati, sai na tafi Najeriya wajen harakokina, kenan ba ya yiyuwa». Wani na uku ya ce : «Ina iya shiga cika aikin tsabtar gari, amma sai idan a biya ni». |

Malami ya bar mahalartan su yi lissafi, ya sanya, su canza ra'ayi kuma ya takaice hirar. Ya kamata ya kwatanta masu da cewa, sai idan mambobi suna iya bayar da kansu, kuma suna da samun dama don shiga cikin aikace-aikace. Kuma ya kwatanta da cewa, su mambobin biron suna aiki don ci-gaban gari.

| |
|---|
| An gayyaci taro don a mizanta aikace-aikacen da aka aikata cikin wata. Dukan mambobi su halarta wurin taron a lokacin amma shugaban sai bayan awa ɗaya ya iso. Ya ce ma mataimakinshi, ya shugabanci taron ,saboda shi, wajen taron ƙungiyar siyasarshi za shi tafiya. |

Karamar wasan kwaikwaya ta biyu

Malami ya tambayi mahalartan : yaya kuka ga halin wannan shugaban ? Waɗanne irin halaye suka dace da shugaba ? Malami ya takaice hirar, kuma ya yi bayani da cewa, shi matsayin shugaba, da matsayin mataimakinshi ,suna tare da bayar da kai kuma da samun dama duk lokaci.

Ƙaramar wasan kwaikwayo ta uku

| |
|---|
| Ga wani taron biro, shugaba ya tambayi magatakarda ya karanta rubutacce bayanin taro na baya. Magatakardan ya fara tambaya mutane, su tuna mashi abin aka ce cikin babban taron da ya wuce. |

Malami ya tambayi mahalartan : yaya kuka ga halin wannan magatakardan ? Waɗanne irin halaye suka dace da magatakardan biro ? Malami ya takaice hirar, kuma ya yi bayani da cewa, shi matsayin magatakarda da mataimakinshi, sai ala tilas mutanen da suka iya karatu da rubutu.

Ƙaramar wasar kwaikwayo ta huɗu

| |
|---|
| Ga babban taro, an ɗauki matakin a yi cikaro-cikaro na dala tamanin ,duk ga kan kowane gida, don a gina rijiya. Ma'aji kuɗi ya karɓi kuɗin cikaro-cikaron ,amma ba inda a yi rubutu, sai ya sa su cikin aljihunshi. Zuwa can sai ya sayi dabino da paken attayi da kuɗin da suke cikin aljihunshi. |

Malami ya tambayi mahalartan : yaya kuka ga halin wannan ma'ajin kuɗi. Waɗanne irin halaye suka dace da ma'ajin kuɗi ?
Malami ya taƙaice hirar, kuma kwatanta sharuɗɗa da ya kamata a cika kafin a zama ma'ajin kuɗi ko mataimakinshi: wato sai ala tilas, an iya karatu da rubuta da kuma iya lissafi sosai. Bayan haka, ya kamata a ce mutum yana da iyauci da bin sassala.

Haka ,su ma masu bincike, ya kamata a ce, suna da waɗannan halayen irin na ma'azan kuɗi.

14) Malami ya nuna cewa ya cancanta, a kafa wani kwamitin zaɓe mai zaman kanshi, kuma ya tayar da babban taron don kafa shi.
    Wannan kwamitin ya ƙumshi: shugaba 1, magatakarda 1, da ɗaya daga cikin mataimakan. Mambobin kwamitin ba su iya yin takara.

15) Malami ya bayyana ma mambobin kwamitin ayyukansu.

16) Kwamitin yake ɗaukar sunayen masu takara. Malamin ya jayo hankalin mahalartan cewa ,su yi aiki da kowa da kowa (attajiri ko talaka, barwai, namiji ko mace). Ya goyi bayan mata, don su yi zaɓe, su yi takara kuma a zaɓe su ga manyan miƙamai (a ƙalla mace biyu cikin kowane buro).

17) Kwamitin ya tambayi taron babbar majalisa, ta ƙayyade rana, da wuri, da lokacin zaɓen (a duba lokacin da za a fi samun mutane, maza da mata). Kar mata su yi kaɗan. Malami ya ƙara jan hankali don mata su zo da dama wurin taron babban majalisa.

**Jan hankali** : Malami ya bayyana ma masu takara cewa, kar su yi jiran wani tukwici daga hurojen ( alawus ko wata kwangila).

18) S'an nan ne malamin da kwamitin zaɓen za su yi ma kowa godiya kafin su rufe taron.

## Mataki na 3 : Shirin kayan aiki a jajibirin ranar zaɓe.

Malami za ya taimaka ma kwamitin zaɓen, don tafiyar da zaɓen da kyau, ta waɗannan hanyoyin :

- ƙera akwatin ƙuri'a ;
- buga ƙuri'o'i (kowane ɗan takara yana da launinshi) dangance da adadin masu zaɓe;
- shirya makewayar zaɓe (malaɓa);
- shirya kwandon shara;
- shirya irin (siffar) takardar rubutaccen bayyani (ruhoto);
- shirya ambalani (su fi yawan mahalarta taron farko na taron babban majalisa);
- shirya takardar sunayen masu zaɓe.

## Mataki na 4: Taron babbar majalisar zaɓe

**Jan hankali**: a wannan matakin, aikin malamin, shi ne,ya riƙa dubawa idan zaɓen yana gudana da kyau.

1) Kwamitin ya duba idan an kawo duka kayan aikin (ƙuri'u, da ambalan, da rumfar ƙauyacewa, da akwatin ƙuri'a, da takardun rubuta sunayen masu zaɓe, da takardar rubutaccen ruhoto).
2) Kwamitin ya riƙa rubuta sunayen masu zaɓen, ɗaya bayan ɗaya.
3) Kafin a fara zaɓen, kwamitin ya ɗauki mataki game da waɗanda suka makara.
4) Kwamitin ya karanta sunayen masu takarar; kuma idan babu ɗan takara ga wani matsayi ko miƙami, sai ya nemi wani ɗan takarar don a cike takardar sunayen.
5) Ga kowane matsayi, ya kamata kwamitin ya karanta sunayen masu takarar, ya gabatar da su.

Kowane ɗan takara za ya bayyana mafarin takararshi, kuma ya gabatar da launin ƙuri'arshi.

6) Kwamitin ya nuna kangon akwatin ƙuri'un da malaɓar.

7) Kwamitin ya nuna yadda ake gudanar da zaɓen.
Magatakardan kwamitin yake kiran masu zaɓen, kuma mataimakan suna miƙa masu ƙuri'un da ambalan (haka ya fi sauri). Masu zaɓe su jera.

Kowane ɗan zaɓe za ya ɗauki ambalan guda, da ƙuri'a a cikin kowane tulin ƙuri'u (kowane tuli, na wani ɗan takara ne). Idan ɗan takara guda ne kaɗai ga wani matsayi, zaɓen » i » ko » a'a » ne.

Idan ɗan zaɓe ya shiga malaɓa, sai ya sanya ƙuri'a guda da ya zaɓa a cikin ambalan ba ta tare liƙe ta ba. Sa'an nan, ya zubda sauran cikin kwandon shara (ko buhu), ya fito.

Idan ya fito, sai ya je ya sanya ambalan ɗin, cikin akwatin ƙuri'a da yake gaban kwamitin zaɓe. Magatakardan kwamitin yake kurce gaban sunan wanda ya yi zaɓen.

8) A ƙarshe, sai kwamitin ya fara ƙilgon ƙuri'u :

- Ya kwatanta adadin ɟan zaɓen da na ambalappopin.
- Ya buɗe ambalappopin gaban kowa da kowa.
- Ya keɓe ƙuri'un launi launi
- Ya ƙilga ƙuri'un kowane ɗan takara
- Ya faɗi sakamakon zaɓe. Idan an yi kunnuwan doki, sai a shirya zaɓen zagaye na 2 tsakanin ɟan takarar 2 da suka zo na farko, a makon gaba.
- Ya gabatan da wabda ya ci zaɓe.

Kwamitin ya gabatar da sabon biron kuma shugaban ya yi jawabinshi.

9) A ƙarshen duka ayyukan,duka mambobin kwamitin suke sa-hannu ga rubutaccen ruhoton zaɓen.

10) A ƙarshe, sai kwamitin ya yi ma mahalartan godiya.

11) Malamin ya tabbatar da takardar masu zaɓen, da takardar ruhoton an ruɓanya su sau uku-uku, kuma an miƙa su ga abokan hulda (garin, da kwamin ɗin garin, da ƙungiyar binciken dausayoyin yankin Sahel.)

Misalin takardar sakamakon zaɓen mambobin (na biron) komitin garin na ci-gaba.

Garin…………………………………..komin ɗin …………………………………………….

Shekarar alif dubu biyu …………. ta rana kaza ……………… a ƙarfe………………

Cikin gidan …………………. an yi babban taro na biyu na mutanen garin………………

(komin ta...........) domin a yi zaɓen biron kwamitin garin na ci-gaba.

- Shugaban biron zaɓe
- Da magatakardan biron zaɓe
- Da mataimaki na farko
- Da mataimakn na biyu

A ƙarshen wanen zaɓen, an zaɓi mambobin biro na CVD.

Ga sakamakon zaɓen:

- Shugaba.................................................
- Mataimakin shugaba.................................
- Magatakarda..........................................
- Mataimakin magatakarda............................
- Mai asusun kuɗi.........................................
- Matimakin mai asusun kuɗi……………………………….
- Mai watsa labaru…………………………………………………
- Wakiliyar mata…………………………………………………
- Wakilin matasa…………………………………………………
- Wakilin manoma…………………………………………………
- Wakilin makiyaya……………………………………………..
- Wakilin ma'aikatan hannu……………………………………
- Masu larwai na asusun kuɗi (waɗanda ba su cikin biro ba).

An rubuta wannan ranar……………………………..

A garin.................................................

Shugaban biro na zaɓe.



1) Waye kai bisa tsarin tashi da kanka, kuma da bayar da bayani a kan ayyukan mambobin biron CVD lokacin babban taro na farko.

2)Wani mamban kwamitin zaɓe yana gwada kwamitin zaɓen mai zaman kanshi, kuma yana bayar da bayani da yadda ake tafiyar da zaɓen.



3) Masu takara na wani matsayi, sunagwada ƙuru'o'insu.





4) Wani mai zaɓe cikin runfar ƙauyacewa, ga wani zaɓen biron CVD.




5) Wata mai zaɓe tana tsakar sanya ambilan cikin akwatin ƙuru'a.